# TASIRIN ‘YARKASUWA A GARIN SIFAWA

**NA**

***HABIBU BALARABE SIFAWA***
**ADM.NO: 1011106001**

**KUNDIN BINCIKE NA SHAIDAR KAMMALA KARATUN DIGIRIN FARKO (B.A HAUSA) DA AKA GABATAR A SASHEN NAZARIN KOYAR DA HARSUNAN NAJERIYA JAMI’AR USMANU [ANFODIYO SAKKWATO**

**NUWAMBA, 2015**

## TABBATARWA

Na amince da kundin bincike na Habibu Balarabe Sifawa, mai lamba 1011106001. Ya cika duk irin }a'idojin kammalawa da aka shimfi]a ]angane da neman takardar digiri na farko (B.A Hausa) a sashen Harsunan Najeriya na Jami'ar Usmanu [anfodiyo Sakkwato.

---------------------------------------- ------------------------

Malam Rabi'u Aliyu Rambo Kwanan Wata

(Sa Hannu mai dubawa)

---------------------------------------- ------------------------

Farfesa Abdullahi M. Dantumbushi Kwanan Wata

(Sa Hannun Shugaban Sashen)

---------------------------------------- ------------------------

Kwanan Wata

(Sa Hannun mai dubawa na Waje)

## SADAUKARWA

Ina mai sadaukar da wannan aiki ga kakata wanda Allah ya yi wa rasuwa shekara biyu da suka wuce. Ina ro}on Allah Ya gafarta mata kurakuranta amin. Bayan haka ina sadaukar da wannan aiki ga mahaifana Balarabe Yari Sifawa da mahaifiyata Hauwa'u.

# GODIYA

Godiya ta tabbata ga Allah ma]aukakin sarki, mai kowa mai komai, mai yanda ya so, yayin da ya tabbata ga Allah ma]aukakin sarki mai ba kowa komai ba shi bu}atar komai a wurin kowa, kowa nada bukatar komai a gare shi. Mamallakin mamallake mai bada mulki ga wanda ya so, ya fizge daga wanda ya so, ya ]aukaki wanda ya so, ya kazkantar da wanda ya so. Sarkin da ba ya da farko ba ya da }arshe, na farko ne ba na }arshe ba da }arewa ba. A bayyane yake ba a ganinsa. A ]aya yake ba don baya nan ba. Sarkin da ya kasance tun kafin kasancewa ta kasance, kuma zai kasance bayan kasancewa ta gushe da kasancewarsa.

Tsira da aminci su tabbata ga Manzonsa (S.A.W) Dan Abdullahi shugaban manzanni cikamakin Annabawa, babban masoyin Allah, babban bawan Allah ba a yi ba ba za a yi kamarsa ba. Da alayensa da sahabbansa da duk wa]anda suke biye da shi zuwa ranar alkiyama. Da farko zan mi}a cikakkiyar godiya ta ga mahaifana Balarabe Yari Sifawa da mahaifiyata Hauwa'u dangane da tarbiyar da suke yi a gareni, tare da kulawa, wanda har na kawo wannan matsayin.

Bayan haka ina mai matu}ar godiya ga malamai na, na sashen koyarda harsunan Najeriya, a Jami'ar Usmanu [anfodiyo gaba ]ayansu, musamman malamina malam Rabi'u Aliyu Rambo, wanda ya jagoranci ]awainiyar duba wannan aiki nawa da han}urin kai da kawo da nake a wurinsa, Allah ya saka da alhairi kuma ya ja kwanansa a gaba sannan ya sanya makwanankinsa albarka, ya ji}an iyayensa. Allah ya albarkaci bayansa. Amin.

Godiya ta musamman ga iyayena da 'yan'uwa na da kuma }anne musamman Alh. Maniru da Alh. Mansur da Alh. Bilyaminu da Alh. Shafi'u da Alh. Surajo da sauransu.

Ba zan manta da irin gudummuwar da suka bani ba, da addu'ar da suke yi mani ta fatr alheri. Bayan haka, ina mai matu}ar godiya ga malamaina irin su Malam Mustafa Umar da Malam Dano Balarabe Bunza da Malam Naziru Umar da Malam Sama'ila Umar Zariya da Malam Zayyanu Abubakar da sauransu. Ba zan manta da abokaina na karatu ba irin su Bashar Tambuwal da Bashar Umar Kaura da Alhassan Ibn Ibrahim da Jamilu Ma'auya Zamfara da Alyasa'u Kano da Ibrahim Dogo da dukkanin abokaina da 'yan

uwana da abokan arziki wa]anda ban ambata ba ina godiya }warai da gaske na gode.

## {UMSHIYA

Taken bincike i

Tabbatarwa ii

Sadaukarwa iii

Godiya iv

{umshiya vii

## BABI NA [AYA: GABATARWA

1.0 Shimfi]a 1

1.1 Bitar Ayyukan Da Suka Gabata 3

1.2 Hujjar Ci Gaba Da Bincike 8

1.3 Hanyoyin Gudanar Da Bincike 11

1.4 Muhalin Bincike 12

1.5 Manufofin Bincike 12

1.6 Na]ewa 13

## BABI NA BIYU: TAKAITACCEN TARIHIN 'YARKASUWA

2.0 Shimfi]a 15

2.1 Tarihin Garin Sifawa A Takaice 16

2.2 Ma’anar ‘Yarkasuwa 19

2.3 Dalilin Zuwan Su Cin Kasuwar 21

2.4 Garuruwa Ko Kauyukan Da Ke Cin ‘Yarkasuwa 22

2.5 Na]ewa 23

**BABI NA UKU: NAU’O’IN KAYANDA A KE SAYA DA SAYARWA A ‘YAR KASUWA**

3.0 Shimfi]a 25

3.1 Kayan Abinci 26

3.1.1 Shinkafa 26

3.1.2 Gero 27

3.1.3 Masara 27

3.1.4 Dawa 28

3.1.5 Maiwa 28

3.1.6 Hatsi/Damma 29

3.1.7 Wake 29

3.1.3 Gya]a 30

3.2 Kayan Miya 30

3.2.1 Tumatur 31

| | | |
|---|---|---|
| 3.2.2 | Tattasai | 31 |
| 3.2.3 | Tarugu | 31 |
| 3.2.4 | Albasa | 32 |
| 3.2.5 | Alayyahu | 32 |
| 3.2.6 | Sure | 32 |
| 3.2.7 | Kabushi/Kabewa | 33 |
| 3.3 | Kayan Marmari | 33 |
| 3.3.1 | Ayaba | 34 |
| 3.3.2 | Lemun Yami | 34 |
| **3.3.3** | Lemun Zaki | 35 |
| **3.3.4** | Karas | 35 |
| 3.4 | Dabbobi | 35 |
| 3.4.1 | Shanu | 36 |
| 3.4.2 | Raguna | 36 |
| 3.4.3 | Akuyoyi | 37 |
| 3.4.4 | Kaji | 37 |
| 3.5 | Sutura | 37 |
| 3.5.1 | Shaddodi | 38 |
| 3.5.2 | Atamfa | 38 |

3.6 Sana'o'in Da Suka Yi Fice A Kasuwar 39

3.6.1 Sana'ar Sayarda Nama (Rundawa) 39

3.6.2 Kayan Gwari (Kayan Miya) 39

3.6.3 Sana'ar Sakai 40

3.6.4 Sana'ar Shayi Da Burodi 40

3.7 Na]ewa 41

**BABI NA HU[U:**

**TASIRIN KASUWAR 'YAR KASUWA A GARIN SIFAWA**

4.0 Shimfi]a 43

4.1 Amfani Da Ake Samu A Cikin Kasuwar 44

4.1.1 Ana Shigowa Da Abubuwan Da Ba Bu Su A Cikin Kasuwar Garin 44

4.1.2 Matasa Suna Samun Aikin Yi A Cikin Kasuwar 45

4.1.3 Ci Gaban Garin Sifawa 45

4.2 Matsalolin 'Yar Kasuwa 46

4.2.1 Rashin Wutar Nepa (Lantarki) 46

4.2.2 Rashin Tallafi Daga Gwamnati 47

4.2.3 Rashin Ruwan Fanfo 47

4.2.4 Rashin Ofishin Yan Sanda A Cikin Kasuwar 48

4.3 Na]ewa 48

## BABI NA BIYAR

## TA{AITAWA DA KAMMALAWA


| | | |
|---|---|---|
| 5.0 | Shimfi]a | 50 |
| 5.1 | Ta}aitawa | 50 |
| 5.2 | Kammalawa | 53 |
| | Manazarta | 56 |

# BABI NA [AYA:

# GABATARWA

## 1.0 SHIMFI[A

Sha'a nin kasuwanci sha'ani ne mai matu}ar muhimmancin gaske ga rayuwar al'ummar Hausawa baki ]aya. Ita kuwa kasuwa muhalli ne da ake saye da sayarwa domin biyan wasu bukatoci na rayuwar yau da kullum. Wannan bincike mai taken "Tasirin 'Yar Kasuwa ga Al'ummar Hausawan Sifawa". Za a yi }o}arin bayanin irin rawar da 'yar kasuwa ta taka wurin bun}asa tattali arziki al'ummar Hausawa a garin Sifawa.

A }o}arin cimma manufar wannan aiki, an kasa aikin zuwa manya-manyan sassa (babi) guda biyar domin samun saukin aikin kamar haka. A babi na farko mai suna gabatarwa yana da }ananan sassa guda shida, wa]anda suka ha]a da sashe mai lamba 1.0 Gabatarwa da 1.1 Bitar ayyukkan da suka gabata da 1.2 Hujjar ci gaba da bincike da 1.3 Hanyoyin gudanar da bincike da 1.4 Muhallin bincike, da 1.5 Manufar bincike sai 1.6 Na]ewa.

A babi na biyu kuwa mai suna "Ta}aitaccen Tarihin 'Yar kasuwa". A nan babi na da }anana sassa guda hu]u wa]anda suka

ha]a da 2.0 Shimi]a da 2.1 Tarihin garin Sifawa a ta}aice da 2.2 da 2.3 Garuruwan da ke cin kasuwar sai kuma 2.4 Na]ewa.

A babi na uku kuma mai taken nau'o'in kayan da ake saya da sayarwa a 'yar kasuwa. Wannan babi an kasa shi zuwa babi shida kamar haka: 3.0 Shimfi]a sai 3.1 kayan abinci a 'yar kasuwa, da 3.2 kayan miya a 'yar kasuwa sai 3.3 kayan marmari a 'yar kasuwa da kuma 3.4 dabbobi 'yar kasuwa, da 3.5 sutura 'yar kasuwa. Sai kuma sashen }arshe wanda ya yi bayanin kayan da aka fi samu a cikin 'yar kasuwa ke nan 3.6 sai 3.6.5 na]ewa.

Bayan haka akwai babi na hu]u wanda ake masa suna "Tasirin kasuwar 'yar kasuwa a garin Sifawa" shi wannan babi an kasa shi zuwa sassa daban-daban a cikin babin. Na farko 4.0 Shimfi]a, sai kuma 4.1 amfanin da ake samu a cikin kasuwa'yar kasuwa 4.1 shigowa da abubuwan da babu su a cikin kasuwar garin, 4.1.2 matasa suna samun aikin yi a cikin kasuwar garin, 4.1.3 ci gaban garin Sifawa baki ]aya.

4.2 matsalolin 'yar kasuwa, 4.2.1 rashin wutar lantarki (NEPA), 4.2.2 rashin tallafi daga gwamnati, 4.2.3 rashin ofishin 'yan sanda a cikin kasuwar, 4.2.5 Na]ewa. Sai babi na biyar wannan

sashen ya nada sashe har hu]u a cikinsa. 5.0 Shimfi]a 5.1 Ta}aitawa, 5.2 Sakamakon bincike, sai 5.3 Kammalawa.

## 1.1 BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA

Har wa yau a cikin wannan aiki za a ta~o wasu aikace-aikace da suka gabata masu dangantaka dangane da wannan bincike wato harakar kasuwanci a cikin 'yar kasuwa ta garin Sifawa. A ha}i}anin gaskiya an ]an yi wasu ayukka wa]anda suka danganci wannan fanni, amma sun sha banban da wannan. Saboda a cikin bincike binciken da na yi na ci karo da wasu kundaye na digiri wa]anda aka gabatar makamantan wannan aiki kuma sun taimaka wajen assasa wannan bincike.

Bincike na farko da aka duba na wani ]alibi mai suna Umar M. (2005). A cikin aikinsa mai taken "Kasuwanci muhimmancinsa ga al'umma Hausawa". A kundin digirinsa na farko. A sashen nazarin harsunan Nijeriya na Jami'ar Usmanu [anfodiyo ta Sakkwato. Wnanan ]alibi ya dubi wane ne ]an kasuwa da kuma ma'anar kasuwanci a al'umma. Bayan haka ya dubi irin kayan da ake sayarwa a cikin kasuwa da huldayyar da Hausawa ke yi da wasu al'ummomi daban-daban. Ya kuma dubi matsayin kasuwanci a yau.

Bugu da }ari ya kawo dangantakar kasuwanci da al'ada inda ya dubi wasu sana'o'in Hausawa da ake samu a cikin kasuwanni da kuma yadda ake aiwatar da su a cikin kasuwanni.

Bayan haka wannan ]alibi ya dubi kasuwanci da kuma bun}asarsa ga al'umma, a nan idan aka dubi aikin wannan ]alibi ya so ya yi kama da wannan domin ya kawo ire-iren abubuwan da ake sayarwa a cikin kasuwa da ma'anar kasuwa, da hul]ayyar da Hausawa ke yi da wasu al'ummomi daban-daban da sauransu. Don haka, aikin ya banbanta da wannan aikin domin an mai da hankali ne ga tasirin 'yar kasuwa a al'ummar garin Sifawa ne a wannan bincike.

Bayan haka, bincike na biyu da aka yi na wani ]alibi mai suna Gali (1986). A cikin aikinsa mai suna "KASUWANCI DA DA NA YANZU A BIRNIN KANO". A kundin digiri na farko, a Sashen Nazarin Harsuna Najeriya na Jami'ar Usmanu [anfodiyo ta Sakkwato. A cikin aikinsa ]alibin ya dubi tsarin cikin birnin Kano ya kuma kawo yadda ake fara yin kasuwanci a cikin birnin Kano da kuma fataken da suke shigowa a cikin birnin Kano don su yi kasuwanci wa]anda aka bar yayinsu wato sun tsufa ambarcinsu misali; Kasuwar Sabon Gari, Kasuwar Kwari. Bayan haka, ya kawo

sababbin kasuwani da suke tashi a birnin na Kano, kamar Kasuwar }ofar Wanbai, Kasuwar }ofar Ruwa, sai Kasuwar }ofar Na'isa da kuma Kasuwar 'Yar Kaba.

Bayan haka, ]alibin ya yi }o}arin kawo wasu sana'o'in da ake yi kamar irinsu }ira, jima, dukanci, da kuma rini. Ya kawo tarihin zuwan Turawa tare da shigowar kasuwanci a birnin na Kano. Abin lura a nan, wannan aikin na wannan ]alibi yana da alaka da nawa domin ]alibin ya kawo tarihin birnin Kano har lokacin da turawa suka zo suka fara yin kasuwanci. Wannan ya }ara mani }arfin guiwa ya sa na yi bincike na kafuwar 'yar kasuwa a garin Sifawa. Don haka ayyukan namu sun yi kama domin duk suna magana ne a kan kasuwanci daga wani sashen }asar Hausa.

Bugu da }ari, an yi bitar bincike na wani ]alibi mai suna Bello (2004). A cikin aikin sa mai suna "NAZARI A KAN KASUWAR KARA TA SAKKWATO. A cikin kundin digirinsa na farko, a Sashen Nazarin Harsunan Najeriya na Jami'ar Usmanu [anfodiyo ta Sakkwato. A cikin wannan aikin na wannan ]alibi, ya yi }o}arin kawo ma'anar kasuwanci da kuma yadda ma'anar kara ta samo asali da kuma kasuwanci dabbobi da ire-iren dabobin da ake sayarwa a

cikin kasuwa ‘yar kasuwa ta kara. Bayan haka, ]alibin ya yo tsokaci kan muhimmancin kasuwar kara a cikin al’umma da shuwagabanninta, ya kuma dubi irin ba}in mutanen da suke kawo dabbobi a cikin kasuwar domin su sayar da su.

Wa]annan ba}i sun ha]a da mutanen Nijar da mutanen Kebbi. [alibin ya yi }o}arin kawo ta}aitaccen tarihin birnin Sakkwato. Wannan aikin na wannan ]alibi ya so ya yi kama da nawa domin mun yi tarayya wajen kawo tarihin gari da abubuwan da ake samu a cikin kasuwa da take ci, da sauransu. Sai dai shi yana magana ne a kan kasuwar kara, wannan aikin kuwa yana nazari ne a kan kasuwar ‘yar kasuwa ta garin Sifawa.

Bayan haka, wani bincike da na yi bita shi ne na wani ]alibi mai suna Aliyu (2011). A cikin aikin sa mai taken: “HARSHEN KASUWANCI NA GIDA DA NA BAKI A KASUWAR, ALBASA TA ALERU”. A kundin digirinsa na farko a }ar}ashin Sashen Nazairn Harsunan Najeirya na Jami’ar Usmanu [anfodiyo ta Sakkwato. [alibin ya kawo ma’anar kasuwanci da kawo tarihin kasuwancin Bahaushe da kuma muhimmanci kasuwanci ga al’umma. [alibin ya kawo ha~akar tattalin arzikin }asa. Bayan haka

ya kawo cewa, kasuwanci kariya ne daga zaman kashe wando ya yi tsokaci kan wasu karuruwan harshe da ake samu sanadiyar kasuwanci. Ya kuma ce, kasuwanci yana raya }auyuka har ma da birane, ya kuma kawo ta}aitaccen tarihin garin Aleru da kuma kasuwar albasa da ke garin na Aleru. Bugu da }ari ya kawo yanayin kasuwanci a }asar ta Aleru, da }ir}irar sababbin kalmomi a cikin harshen kasuwanci gida da na ba}i ya kawo dalilin samuwar sababbin kalmom a harshen kasuwanci harwa yau ]alibin ya kawo nau'o'in kalmomin }ir}ira a harshen kasuwanci da kuma muhimmancin }ir}irarrun kalmomi wajen harshen kasuwanci. Idan muka dubi aikin wannan ]alibi suna da kama da nawa wajen kawo tarihin gairn da kasuwar albasa da ke Aleru da ma'anar kasuwanci da kuma alfaninsa ga al'umma. Sai dai inda muka sha ban-ban da shi ni zan yi maganar ne kawai kan 'yar kasuwa a garin Sifawa, amma duk ayukkan namu su na da kama da juna domin suna magana ne a kan kasuwanci.

Har wa yau, akwai wasu ]alibai da suka yi wani bincike a kan "HAUSAR WASU KEBABBAN SANA'O'IN HAUSAWA KULI DA AWO". Wa]annan ]alibai sun ha]a da Adamu Zakari da

Muhammad Argungu (2010). A kundin digirinsu na farko a Jami'ar Usmanu [anfodiyo ta Sakkwato. A cikin aikin wa]annan ]alibai sun yi }o}arin kawo ma'anar sana'a da kasuwanci da tarihin samuwar sana'a bayan haka sun yi }o}arin kawo ire-iren sana'o'in Hausawa.

## 1.2 HUJJAR CI GABA DA BINCIKE

Ko shakka babu akwai hujjoji masu karfi da suka bani }arfin gwiwar wannan bincike.

Da farko dai dukkan ayyukan da na yi bita ba su ce komai game da 'yar kasuwa ta garin Sifawa ba, duk da yake wasu daga cikin ayyukan da aka yi bita sun shafi al'amurran saye da sayarwa ne waton kasuwanci a wasu sassan }asar Hausa. Misali aikin Umar (2005), ya yi bincike ne a kan "Kasuwanci da muhimmancinsa ga al'ummar Hausawa". Aikin bai ce komai ba game da 'yar kasuwa ta garin Sifawa ba, don haka ya zama hujja a kan aiwatar da wannan aikin.

Haka shi ma aikin Gali (1986), ya yi bayani kasuwanci da ake a da, a wasu kasuwanni Birnin Kano da kuma wa]anda ake cinsu a yau. Haka ya yi bayani irin nau'in kayan da ake sayarwa da kuma masu zuwa cin kasuwar da sauransu. Rashin cewa komai game da

‘yar kasuwar Sifawa ya zama hujja ga ci gaban wannan bincike. Har wa yau wani bincike wanda wani ]alibi ya mai suna Aliyu (2011). Wannan ]alibi ya yi bayani ne kawai dangane da “Harshen kasuwanci na gida da na ba}i a kasuwar Albasa wadda ke Aleru”. Inda ya yi bayanin yadda ake samun sa~abbin wasu harsuna da ake yin kasuwanci. Hujjar ci gaba da bincike shi ne bai ta~a tasirin ‘yar kasuwa wanda take garin Sifawa ba da irin ci gaban da ta samun da nau’in irin abubuwan da ake samu a cikinta, ta gefen kayan abinci da kayan marmari da sauransu ba.

Wata hujja kuwa idan aka kalli aikin Adamu da Muhammad Argungu, mai taken “Hausar wasu ke~a~~an sana’o’in Hausawa kuli da awo”. Wa]annan ]alibai sun yi bayani ne kawai a kan waus kebatattun wasu sana’o’in Hausawa wanda ya shafi ‘yar kasuwa ba da sana’o’in da ake yi a cikin ‘yar kasuwa da ke garin Sifawa.

Bayan haka, sun kawo yadda ake sarrafa yin }uli-}uli da kuma kawo yadda masu sayar da }uli-}uli suke maganarsu. Sun kawo ma’anar awo da yadda ake yinsa. Wannan aikin na wa]annan ]alibai yana da ala}a da nawa domin sun tabo ire-iren wasu sana’o’in Hausawa sai dai wannan aikin ya ke~anta ne kawai a ‘yar kasuwar

da ke garin Sifawa wanda ba su yi magana a kansa ba rashin yin haka, ya zama hujjar aiwatar da wannan bincike.

Akwai wani ]alibi mai suna Aliyu Gada (1989). A cikin aikin sa mai suna “SANA’AR SA{AR KABA A {ASAR HAUSA”. A cikin kun]in digirinsa a sashen Nazarin harsunan Najeirya na Jami’ar Usmanu [anfodiyo ta Sakkwato. Wannan ]alibin ya yi }o}arin kawo ]aya daga cikin sana’o’in Hausawa, ya kawo ]an ta}aitaccen tarihin Hausawa, da kawo ma’anar sana’ar da muhimmancin ta ga al’umma da ita kanta sana’ar kaba da irin kar~uwar da ta samu a al’ummar Hausawa, da dangantakar sana’ar kaba da sauran wasu sana’o’in.

Ya kawo muhimmancin kasuwanci ga al’umma da kawo wasu sana’o’in Hausawa a Sakkwato. Bayan haka, ya kawo ire-iren kasuwanci ga al’ummar Hausawa Kamar Fatauci da Noma, da {ira, da Jima da sauransu.

Wannan aikin na wannan ]alibi ya sha banban da nawa domin a wannan aiki ya ke~anta ne kawai a ‘yar kasuwar garin Sifawa da kuma irin abubuwan da ake samu a cikin ‘yar kasuwa da ke garin na Sifawa da irin ci gaban da ta samu da matsalolin da ke damunta duk an tabo su a cikin wannan aikin.

## 1.3 HANYOYIN GUDANAR DA BINCIKE

Kowane irin bincike da za a gudanar dole a samu hanyoyi na musamman da ya kamata a bi domin cimma nasarar gudanar da wannan bincike. Don haka, a }o}arin gudanar da wannan binciken an yi amfnai da hanyoyi da dama kamar haka.

An yi amfani da mayan kundayen digiri domin tattaro bayanai masu dangantaka da wannan aikin bincike da ke cikin dangane da kasuwanci bayan haka an yi amfani da littattafai da aka wallafa dama wa]anda ba a wallafa ba, domin tattaro bayanai. Har wa yau, kuma an yi amfani da dubarun yin tambayoyi, daga cikin wa]anda ake yi wa tambayoyin akwai dattijai da wasu 'yan kasuwar garin Sifawa. Bayan haka, akwai bu}atar da ta sanya aka duba mujallu da }asidu da jaridu uwa uba kuma tambayar malammai da dai sauran wasu al'umma da suka da ce a tambaya da duk domin zakulo bayanai masu muhimmanci da shawarwari domin cimma nasarar wannan aiki bincike.

## 1.4 MUHALIN BINCIKE

A gaskiya dai “ko mai na da iya ka amma banda ikon Allah”. Dan haka, ya zama dole a bayyana iyakar farfajiyar wannan aiki, domin haka ne za a iya bada haske ga mai karatu saboda ya iya fahintar inda aka nufa. Wannan bincike fa]insa bai wuce yadda aka ambato ba a tun can farko cewa tasirin ‘yar kasuwa a garin Sifawa. Abin da za a yi a cikin wannan aiki ba zai wuce wa]annan iyakoki ba wa]anda aka ambata ba.

A ta}aice dai farfajiyar wannan aiki ya tsaya ne kurum ga abinda ya shafi kasuwar ‘yar kasuwa a garin Sifawa. A nan aikin zai yi tsokaci ne a kan tasirinta kayan kasuwancinta, masu cin kasuwar da kuma tasirinta ga al’ummar Sifawa baki ]aya. Don haka aikin bai shafi wasu abubuwa da suke wajen wannan kunshiya ba.

## 1.5 MANUFOFIN BINCIKE

Kowane ilmi bincike yana da manufar aiwatar da shi, wannan aikin yana da manufofi kamar haka: Manufar farko ita ce: “shi ne duk ]alibin da zai kammala karatunsa na farko wato digiri na farko. To dole ya yi wani aiki ko bincike kafin a ba shi wannan takarda ta cewa ya kammala digiri wato B.A Hausa. Don haka, cika }a’idar da

jami’a ta gindaya kafin bayar da digiri yana daga cikin manufar wannan bincike. Bayan haka, manufa ta biyu ita ce domin kawo irin ci gaban da ‘yar kasuwa ta garin Sifawa ta samu wurin ci gaban al’ummar Sifawa musamman Hausawa.

Haka kuma, binciken zai taimakawa a samu abin karantarwa da kuma yin nazari harshen Hausa. Haka manufar wannan bincike shi ne za baska hanya ga ]alibai masu sha’awar wannan fanni ta yadda za su aza nasu harsahen binciken na gaba domin za}ulo wasu abubuwa.

## 1.6 NA[EWA

A wannan }aramin sashe mai suna na]ewa mai lamba 1.6, a nan sashen ya yi }o}arin kawo kumshiyar aikin da aka tattauna a cikin babin ne a ta}aice. Babin yana da }ananan sassa guda shida (6) wato daga 1.0 zuwa 1.6. A sashen 1.0 yana da shimfi]a, a nan sashen ya yi bayani kumshiyar babi ne ata}aice. A sashe mai lamba 1.1 ya yi bayanin bitar ayyukan da suka gabata, wannan sashen ya yi bitar wasu ayyukan da ke da danganta da wannan aikin. A sashe mai lamba 1.2 kuma yana da taken Hujjar Ci gaba da Bincike. A nan sashen ya yi bayanin irin dalilin da suka sanya za a ci gaba da

gabatar da wannan bincike. A sashe mai lamba 1.3 kuma mai taken hanyoyin gudanar da bincike, a nan sashen ya yi byanin irin dubarun da aka bi wurin gudanar da wannan bincike wa]anda suka ha]a da amfani da kundayen da littafai da ziyarce-ziyarce gidajen tarihi da tambayoyi da sauransu.

A sashe mai lamba 1.4 kuma mai suna Muhimmancin bincike, sashen ya yi bayani farfajiyar wannan bincike ne inda ya ta}aita bakin iyakar fa]in abinda za a tattaro a cikin aikin baki ]ayansa. A }aramin sashe mai lamba 1.5 kuma mai suna manufofin bincike a nan sashe ya yi }o}arin bayanin manufofin da suka sanya ake aiwatar da aikin bincike (Dalilin Bincike). A }arshe na]ewa mai lamba 1.6. A nan an yi }o}arin kawo kumshiyar babin amma a ta}aice.

# BABI NA BIYU:

# TAKAITACCEN TARIHIN ‘YARKASUWA

## 2.0 SHIMFI[A

Wannan babi na biyu mai taken takaitaccen tarihim ‘yarkasuwa zai yi }o}arin bayanin takaitacen tarihim garin Sifawa ne da ‘yarkasuwar kanta. Don haka an kasa babin zuwa }ananan sassa kamar haka:

A sashe mai namba 2.0 mai taken shinfi]a wannan sashen zai yi }o}arin kawo kumshiyar babi ne a takaice. A sashe mai namba 2.1 kuma, sashen zai yi bayani ne a kan takaitaccen tarihim garin Sifawa sama sama. A sashe mai namba 2.2 kuma sashen zai yi bayani ne a kan ma’anar ‘yarkasuwa kanta. A sashe mai namba 2.3 kuwa sashen zai yi bayani a kan ranakkun da ‘yarkasuwa take ci. A sashe mai namba 2.4 kuwa, sashen na da }udurin bayani a kan dalilin sanya wa]annan ranakku da ‘yarkasuwa take ci. Sai a sashe mai namba 2.5 a nan sashen zai yi bayani ne a kan garuruwan da ke cin kasuwar ‘yarkasuwa, a }arshe babin zai na]e da sashe mai namba 2.6 waton na]ewa. A anan sashen zai yi }o}arin kawo kunshiya abin da babin ya tattauna ne a takaice.

## 2.1 TARIHIN GARIN SIFAWA A TAKAICE

Sifawa na cikin yammacin Afirka wanda wani lokaci ana kiransa yammacin Sudan. Tana da kilomita ashirin da takwas, kudu maso yamma ga garin Sakkwato kuma daga cikinta kafin da bayan mallaka har zuwa }ir}ira sauran }asashen daular. Tana hannun riga $10^0$ Arewa da $14^0$ Arewa da kuma layin longitud $30^0$ 31 kudu da $7^0$ 15 kudu. Wannan bayani an samo su ne a wani littafi mai suna tarihin garin Sifawa kafin jahadi da kuma bayan jahadi, wanda Abdullahi Muhammad Sifawa ya rubuta, wannan bayani za a same shi a feji na talatin da biyar (35) zuwa shafi na hamsin da bakwai (57). Bayan muhimmancin aikin gona, ruwan sama na tsananin wuyar samu. Kuma Hausawa na cewa "Da ruwan sama ake jawo na }asa", saboda muhimmancin ruwa ga rayuwa. Da]i da }ari ma an kula da yanayin rayuwa da siyasa wajan }ir}iro garin sifawa. An ba garin suna ne bayan wanda ya kafa garin waton "Sifawa" wanda an yi imanin ya zo daga Barno. Ya zo garin a matsayin ]an Farauta da ya cimma wurin da wadatan ita ce da kuma namun daji daban daban sai ya kashe wasu ya samu wurin zama ya ci gaba da farauta. Daga

wurin zaman ne ya bun}asa ya zama gari an ba shi sunansa. Babu tsayayyen kwanan wata da ake ganin an samar da garin na sifawa, amma an tabbatar da cewa garin yana }ar}ashin mallakar }asar kabi har zuwan Shehu Usman da mutanensa a garin Sifawa.

Sifawa bayan zuwan shehu Usman [anfodiyo. Shehu Usmanu ya amsa gaiyatar Muhammadu Bello, kafin yabar Sifawa ya bar ]ansa Muhammadu Buhari ya amshi ragamar shugabancin garin Sifawa ga babanai a 1815. Ya ci gaba da zama garin har rasuwar shehu Usman [anfodiyo, ya kasance ya yi karatu ga babansa, sannan da kawunsa shehu Abdullahi bayan ]agawar babansa Shehu Abdullahi ya }ara shakuwa da shi fiye da da.

Bayan Muhammadu Bello ya gaji babansa Shehu Usman [anfodiyo, Muhammadu Buhari ya bi ta wansa Shehu Abdullahi daga Bo]inga zuwa Gwandu kafin su kai Gwandu ya zauna wani gari da ake kira Tambuwal, daga nan ne ya wuce Gwandu ya ci gaba da taimakawa kawunsa ga harakar mulki da kuma karantarwa, wannan shi ne alakar zaman takewar Gwandu da Tambuwal, wanda yake ba su rabuwa siyassance har zuwan turawa har yau, a shekara ta 1850. malam Aliyu ya amshi sarautar daga Muhammadu Buhari shi kuma,

Malam Aliyu Babba (Sarkin Musulmi) ya amshe sarautar Sifawa daga zuwa sarkin sarautar Sifawa daga ajiya zuwa sarkin kudu sannan ya yi mulkin garin daga shekarar 1850 zuwa 1910 lokacin da ya kaura. Bayan rasuwar, Malam Abubakar sahabi ya gaji sarautar tsawan shekara 13, shi kuma daga 1910 zuwa 1923 lokacin da ya amsa }iran Ubangijinsa. Shi kuma ]ansa muhammadu sahabi shi kuma ya gaji karagar mulki ga babansa. Ya mulki }asar tsawon shekara 15 daga 1923 zuwa 1938, Muhammadu ]an Aliyu dan Muhammdu Buhari ]an Usman [anfodiyo. Ya gaji malam ]an Abubakar sahabi a 1938.

Daga baya an canza shi daga Sifawa zuwa hakimin Talatar Mafara. Ya zauna sarkin kudun Sifawa a tsawon shekara hu]u (4) kamin ya rasu shekara 1942. shi kuma ]anshi Umar ]an Mahmud ya gaji sarautar 1942 zuwa 1945. shi kuma shekara arba'in (40) daga 1945 zuwa 1995 lokacin da ya kaura. Yanzu Alhaji Muhammadu Buhari shi ne Sarkin Kudun Sifawa wanda ya gada daga babansa.

Zuwan Shehu Usman [anfodiyo garin na, Sifawa ya tarar da mutane garin na Sifawa suna addini sai dai ya sa~awa wasu }a'idodi na musulunci da wasu abubuwa na bauta, wa]an da suke sabawa

addinin musulunci, duk da haka, sun san akwai jahilci cikin al'ummar garin, domin suna 'yan tsafe tsafe da wasanni har da matan banza wato karuwai. Zuwan Shehu Usman [anfodiyo ya kawo sauyi sosai domin ko duk abubuwan nan na ~arno an bar su aka bu]e makarantu na addinin musulunci don karantar da al'ummar garin na sifawa, saboda tun farko mutanen garin Sifawa musulmai ne sun sami saukin barin duk wani abu wanda ya sa~awa addinin musulunci a nan take.

Mutanen garin Sifawa fulani ne domin kuwa suna kiyon dabbobi da dama kamar Shanu da raguna da awaki kai harma da rakumma suna }iyo, bayan haka ga noma da mutanen garin na Sifawa ke yi domin su sayar su kuma ba dabbobinsu domin kiyon ya yi masu sau}i. Bayan kiyo da noma suna sana'ar sakai da kuma farauta domin }ara bun}asa tattalin arziki garin na sifawa.

## 2.2 MA'ANAR 'YARKASUWA

Wannan suna na 'yarkasuwa ya samu asali ne a saboda mutanen da suke zaune a garin na Sifawa suna sana'o'i, daban sai suka yanke shawarar su dinga ha]uwa wuri ]aya suna kasuwancinsu a wuni wuri daban a cikin garin na Sifawa. Sai suka kama ce ma

ha]arsu ‘yarkasuwa wato }aramar kasuwa wanda bata kai ga babba ba, amma akwai babbata a garin Bo]inga wadda ke ci a duk Talata da Jimu’a a cikin sati. Wato babu wani takammen sunanta Illa suman da aka bata wato ‘yarkasuwa. A kwana a tashi har sunan ya bita, harwa yau, ga al’adar malam Bahaushe, duk wata }aramar kasuwa yakan kirata da suna ‘yarkasuwa saboda ba ta kai ga babbar kasuwa ba.

A wata ganawa da na yi da wasu dattijawa mazauna garin Sifawa sun shaida mani cewa, wa]annan da suka fara kasuwanci, su suka saka mata suna “yarkasuwa” kuma daga cikinsu. Allah ya yi masu rasuwa, kuma bincike bai samu ta}amamen sunayen su ba amma sune asali sunan. Bayan haka babu ta}amnmen shekarar da aka bu]e kasuwar kamar yadda mutanen suka shaida mani.

Dalilin da ya sa aka kafa kasuwar ‘yar kasuwa na farko dai domin a’lumma garin na Sifawa su sami saukin rayuwa waton ya zan duk abinda suke son saya za su same shi a cikin kasuwar ba tare da sun je wani wuri ba. Dalili na biyu kuma shi ne cigaban gari domin gari baya cigaba idan ba’a kasuwanci a cikinsa, amma idan ana kasuwanci al’umma za su kama zuwa cikin shi domin saye da

sayarwa. Abu na uku kama shi ne don matasa su sami abin yi su bar zaman banza a cikin garin domin zaman banza shi ke kawo sace-sace da fa]ace-fa]ace a cikin al'umma. Idan akwai abin yi zai yi maganin duk wannan matsala.

## 2.3 DALILIN ZUWAN SU CIN KASUWAR

Akwai dalilai da yawa da ya sa wa]annan garuruwa ko kauyuka suke zuwa cin kasuwar 'yarkasuwa. Dalili na farko shi ne akwai gero muna da nau'in gero kala uku kamar haka: gajaga, da suna da ]an bana duk nau'in gero ne da ake samu a 'yarkasuwa. Dalili na biyu wa]annan kayan abinci suna da arha sosai da sosai, sa~anin wata kasuwa, in da zaka samu kayan su da tsada, harwa yau, akwai nau'in shinkafa akwai nau'in daban-daban kamar shinkafa fara, shinkafa shanshera shinkafa 'yar}u}uma duk zaka same su a cikin 'yarkasuwa. Idan aka dawo gefen dabbobi kuwa akawai sauki sosai. Dalilin na hu]u da ya sa a ke zuwa cin 'yarkasuwa shi ne akwai kayan gwari masu kyau masu arha da ake samu a cikin kasuwar. Kayan sun ha]a da alaiyahu da tattasai da attarugu duk a anan ake noma su, don haka za su yi sauki sosai. Sai dalili na biyar shi ne garin na Sifawa ana da kamfanin yin jus da ruwan leda,

wannan kamfanin sunansa sagar suna sarrafa jus da ruwan leda. Wannan shi ya sa wa]annan garuruwa da kauyuka suke zuwa garin na Sifawa domin su saya kuma su sayar su sami wani abu wato riba.

Duk wa]annan dalilai shi ya sa kasuwar take ci a koda yaushe ba dare ba rana.

## 2.4 GARURUWA KO KAUYUKAN DA KE CIN ‘YARKASUWA

Kafin ma tsunduma a cikin aikinmu ya kamata a san ma’anar gari da kauyuka. Wato idan aka ce gari yana nufin wuri ne inda mutane ke zaune a cikinsa kuma akwai abubuwa da dama wa]anda ]an adam ya ke more rayuwarsa. Ma’ana akwai abubuwa na jin da]i a cikin gari sa~anin kauye lokukta da yawa mutanen kauye sukan shigo gari domin su samu abin biyan bu}ata na rayuwa. Idan aka ce kauye to a gaskiya rayuwa nada wuya, sai dai han}uri domin duk wani abu na jin da]i sai an kawo maku shi, sa~anin birni, ko gari.

Babu shakka akwai garuruwan da suke ci kasuwar ‘yar kasuwa, bayan haka akwai kananan hukumomi da suke zuwa suna kawo sana’o’insu suna sayarwa ga wa]ansu, kamar }aramar hukumar Yabo da Shagari da kuma Tambuwar. Sai }auyukan da

suke zuwa kamar Dajedi da labani da Abdulsalami da }irgori duk kansu sukan kawo sana'o'in su cikin 'yarkasuwa don su saida su kuma sayo wasu abubuwan da ba su da.

Kamar }aramar hukumar Yabo sukan kawo kaji da Zabbi da Talotalo don su sayar suma su sami wani abu su saya su koma da shi garuruwansu. Sai }aramin hukumar Tambuwal Allah ya albarkace su da dabbobi suma suna kawo dabbobin a cikin 'yarkasuwa domin su sayar dasu, suma idan sun sayar da su sai su sayi wani abu su koma garin na su. Daga nan sai }aramar hukumar Shagari wannan }aramar hukumar Allah ya bata albarkar }asa domin suna noma sosai da sosai suma sukan kawo nasu kayan kamar gero da dawa da wake da maiwa duk a cikin 'yarkasuwa suma su sayar su samu wani abu su saya su koma da shi garinsu. Wa]annan ka]an ne daga cikin }ananan hukumomin da ake zuwa cin kasuwar 'yar kasuwa da nau'in kayan da suke shigowa da su a 'yar kasuwa. Don haka akwai sunansu da dama.

## 2.6 NA[EWA

Wanna sashen mai taken na]ewa ya takaita kunshiyar abin da babin zai yi magana baki ]ayansa amma a takaice kamar haka: A

sashe mai namba 2.0 mai taken shinfi]a, wannan sashen ya kawo kanshiyar babi ne a takaice. A sashe mai namba 2.1 kuma sashen ya yi bayani ne a kan takaitaccen tarihin garin Sifawa sama-sama. A sashe mai namba 2.2 kuma sashen ya yi bayani ne a kan ma'anar yarkasuwa kanta.

A sashe mai namba 2.3 kuma sashen ya yi bayani a kan dalilin sanya wa]annan ranakkun da 'yarkasuwa take ci. Sai a sashen mai namba 2.4 a nan sashen ya yi bayani a kan garuruwan da ke cin kasuwar 'yarkasuwa. A karshe babin zai na]e da sashen mai namba 2.5 waton na]ewa. A nan sashen zai yi }o}arin kawo kumshiyar abin da babin ya tattauna ne a takaice.

# BABI NA UKU:

## NAU’O’IN KAYANDA A KE SAYA DA SAYARWA A ‘YAR KASUWA

### 3.0 SHIMFI[A

Wannan babi na uku mai taken Nau’oin kayan da ake saya da sayarwa a ‘yarkasuwa. Wannan babi na uku zai yi }o}arin kawo nau’o’in kayan da ake saya da sayarwa a cikin yarkasuwa. Dan haka an kasa wannan babi zuwa }ananan sassa daban daban kamar yadda za a gani }asa.

A sashe mai namba 3.0 mai taken shinfi]a wannan sashen zai yi }o}arin kawo kumshiyar babin ne a takaice. A sashe mai namba 3.1 kayan abinci, sashen zai yi bayani da suka ha]a da shinkafa da Gero, da masara da Dawa da Maiwa da hatsi/damma da wake da Gya]a. A sashen mai namba 3.2 kayan miya a nan sashen zai yi bayani kayan miya da suka ha]a da Alaiyahu da sure da tattasay da Tarugu da Albasa da Tomator da kabushi. A sashe mai namba 3.3 kayan marmari, sashen zai ta~o kayan marmari kamar Ayaba da lemun zaki da lemun yami da yalo da karas. A sashe mai namba 3.4 Dabbobi, sashen zai yi bayannin dabbobin da ake samu kamar shanu da raguna da awaki da kaji. A sashe mai namba 3.5 anan za a yi

bayanin irin suturar da ake samu a ‘yarkasuwa kamar haka: shaddodi da atamfofi. A kwai sana’o’in da suke yi fice a kasuwar a sashen mai namba 3.6, a shashe mai namba 3.6.1 rundawa masu sai da nama, a sashe mai bnamba 3.6.2 kayan gwari. A sashe mai namba 3.6.3 Sana’ar sakai. A sashe mai namba 3.6.4 sana’ar sayar da shayi da burodi. Da karshe muna da na]ewa mai namba 3.7 inda za a kawo kunshiyar babbin a takaice.

## 3.1 KAYAN ABINCI

Kayan abinci: - wannan yana nufin irin nau’in kayan abincin da ake samu musamman a ‘yarkasuwar ta garin Sifawa. Abinci kuwa wani nau’in cimaka ne wanda ke da wasu nau’ukan sanadarai masu gini jiki. Abinci shi ne ginshikin samar da rayuwar ga al’umma domin ba tare da abinci ba da wuya a samu rayuwa mai inganci. Don haka, a wannan sashe an yi }o}arin duban irin nau’o’in abinci daban da ake samu a kasuwar ‘yarkasuwa da Hausawa ke amfani da su a garin Sifawa.

### 3.1.1 SHINKAFA

Shinkafa wani nau’in abinci ne da Hausawa musamman mazauna garin Sifawa da kewaye ke amfani da ita wurin sarrafa

cimaka iri daban-daban tun daga Tuwon shinkafa da fura ta shinkafa da dai sauransu. Bisa ga la'akari da irin muhimmancin da shinkafa ke da ya sa a kowane lokaci ka shigo kasuwar 'yarkasuwa za ka sami shinkafa ta sayarwa. Bugu da }ari ana iya samun ta tuwo da shinkafa (mai ~awo) da gumi (ta dafawa). Baya ga wannan ana samun daffafar shinkafa wadda aka riga aka dafa, wadda za a ci da miya ko da yaji.

### 3.1.2 GERO

Shi ma gero wani irin nau'in abinci ne da Hausawa musamman mazauna garin Sifawa da }auyuka ke amfani da shi wajen sarrafa cimaka irin daban-daban tun daga tuwon gero da fura ta gero da dambu duk ana sarrafa gero ta wannan hanya. Bayan haka, akwai nau'in gero da ake samu a cikin 'yarkasuwa da ke garin na Sifawa wanda ya ha]a da gajaga da sabon gero da shakararren gero duk ana samunsu a 'yar kasuwa.

### 3.1.3 MASARA

Ita ma masara, wani nau'in abinci ne da Hausawa su ke amfani da shi musamman mazauna garin Sifawa da kauyukan da suke

kawaye da ita. Ana amfani da masara wajen sarrafa cimaka iri daban daban tun daga tuwon masara da dambun masara da sauransu.

Bayan haka, ana sarrafa ta tare da gero don su bada wani kalar cimaka da ake cewa da furar masara da gero wannan cimaka an fi yinsa idan aka yi yayen yaro, lokacin za a yi shi, domin a rabawa al'umma.

### 3.1.4 DAWA

Dawa wani nau'in abinci ne da Hausawa musamman mazauna garin Sifawa da kewaye ke amfani da ita wurin sarrafa cimaka iri daban-daban tun daga tuwon dawa da furar dawa da dambon dawa, duk za a iya sarrafa dawa a yi wa]annan nau'ukan abinci, harwa yau, ana da ire iren nau'o'in dawa kamar haka: -

Mace da kunya da jar dawa da farar dawa, bayan haka a kan sarrafa sansamunta domin a yi rini da shi.

### 3.1.5 MAIWA

Wani nau'in abinci ne da Hausawa musamman na garin Sifawa da kawayenta suke amfani da ita wurin sarrafa cimaka iri daban-daban tun daga furar maiwa da dambu, maiwa kamar gero ce amma shi gero ya fi girma ita maiwa }arama ce ba ta da girma sosai,

a kwai nau'ukan maiwa daban-daban da ake samu a 'yarkasuwa ta garin Sifawa kamar haka: - yar bana da shekararrar maiwa, da kuma damman duk akwai ta a 'yarkasuwa ta garin Sifawa.

### 3.1.6 HATSI/DAMMA

A nan idan aka ce hatsi ana maganar gero, ke nan, wani suna ne da ake kiran gero da shi wato hatsi amma duk ma'anar ]aya ce. Amma a nan garin Sifawa an fi yawan amfani da kalmar gero, wato karin halshe kawai ya banban ta gero ko hatsi. Shi kuma damma idan aka ce damma anan, ana nufin geron da yake cikin karenshi wato ana ce mata zargarniya, ko kuma geron da ba a sassuke shi ba shi ake cewa damma.

### 3.1.7 WAKE

Wake wani nau'in abinci ne da Hausawa musamman mazauna garin Sifawa suke amfani da shi da duk kauyukan da suke zagaye da garin na Sifawa. Wake ana amfani da shi wajen cimaka iri daban-daban tun daga shinkafa da wake, dafuwar wake zalla, da kuma faten wake, sai wani abincin fulani mai suna "Lulaye" duk nau'in abinci ne da ake sarrafawa da wake. Bugu da }ari, akwai wani abu mai

suna ]anwake da ake sarrafawa da wake a samar da shi duk a cikin garin na Sifawa.

### 3.1.3 GYA[A

"Gya]a mai sihiri a ~ara a ga biyu a murza a ga hu]u a buga a ga shika-shikan da]i na tashi sama" wannan }irarin ne daga bakin fulani. Wannan nau'in abinci ne da Hausawa musamman mazauna garin Sifawa suke amfani da shi domin cimaka a kan sarrafa gya]a zuwa nau'i daban-daban na abinci, da farko dai akwai kunun gya]a da ake yi a kan kuma dafa ta domin a ci, har wa yau a kan sata cikin miya kuma a kan yi miyar gya]a zalla.

## 3.2 KAYAN MIYA

Kayan miya wannan yana nufin irin nau'in kayan miyar da ake samu musamman a 'yarkasuwa ta garin sifawa. Kayan miya suma sukan ta ka tasu rawar domin akwai abinci da baya ciyuwa sai an yi masa miya, miyar kuwa ba ta ha]uwa sai da kayan yin ta wato "kayan miya" ke nan, akwai kayan miyar da sai an sarrafasu akwai kuma wa]anda ba sai an sarrafasu ba, akwai kuma wa]anda ba sai an sarrafa su da alaiyahu da sure da kabushi wa]annan kayan suna bu}atar a dafa su su dafu kafin a cinsu, bayan haka akwai wa]anda

ba sai an sarrafa su ba kamar haka: latas da tumatur da taruggai da tattasai wa]annan kayan za a iya cinsu ba tare da an dafa su ba.

### 3.2.1 TUMATUR

Tumatur wani nau'in kayan miya ne wanda ake sarrafa shi ko kuma a ci shi haka ba tare da an sarrafa shi ba, akwai nau'in tumatur da ake iya samu cikin 'yarkasuwa ta garin Sifawa kamar: ]an e ka da nunar rana da ]an Naija duk zaka same su a 'yarkasuwa ta garin Sifawa kuma al'umma na amfani da su ta fuskoki daban-daban musamman a wajen gyaran abincinsu.

### 3.2.2 TATTASAI

Wani nau'in kayan miya ne shima da akan sarrafa shi, kuma wani lokaci a kan ci shi haka nan ba tare da an sarrafa shi ba. Akwai nau'in tattasay daban daban da za a samu a yarkasuwa kamar haka: akwai tsanwan tattasai, a kwai ja jawur wanda ya fi yaji

### 3.2.3 TARUGU

Tarugu wani anu'iun kayan miya ne shi ma akan sarrafa shi wurin yin abinci suna da kama da tattasai, sai dai tarugu }arami ne sosai da gaske shi ko tarugu yana da yaji sosai idan aka zo sarrafa shi a kan sa shi ka]an a cikin abinci saboda yajinsa.

### 3.2.4 ALBASA

Albasa wani nau'in kayan miya ne da ake amfani da ita wajan yin abinci domin tana gyara abinci. Bayan haka, albasa ana dafa ta a ci domin tana maganin sanyi kuma a kan sarrafa ta wajen yin dambu ana kuma soya mai da ita kamar manja ko man gya]a duk ana amfani da albasa. Akwai ire-iren albasa a cikin 'yarkasuwa da take garin na Sifawa. Kamar haka: akwai albasa mai gabu, akwai maras gabu, akwai shekararriyar albasa, akai mai toto duk nau'in ne na albasa da a ake samu a garin Sifawa a cikin 'yarkasuwa.

### 3.2.6 ALAYYAHU

Wani nau'in kayan miya ne da ake sarrafawa ana amfani da shi wajan yin abinci. A na sarrafa shi a ci shi haka nan, ana kuma yin miyar alayyahu zalla, ana soyashi tare da kwai, bayan haka akan ha]a shi tare da sure a yi miyar su wuri daya.

### 3.2.6 SURE

Nau'in kayan miya ne da ake amfani da shi wajen yin miya. Akwai kuma abubuwa daban-daban da ake yi da shi. Akan yi miyar sa zalla, harwa yau akan yi dambu a sa sure ciki, akan dafa shi a ci shi haka nan zalla. Bayan haka, akwai nau'in sure iri biyu da ake

samu a cikin ‘yarkasuwa ta garin sifawa. Dukkan wa]annan nau’ukan sure Hausawan garin Sifawa na amfani da su wajan sarrafa nau’ukan abinci daban-daban na Hausawa.

### 3.2.7 KABUSHI/KABEWA

Wa]annan abubuwa suna cikin nau’in kayan miya da a ke amfani da su wajen yin miya ko wani abinci na ci. Kabushi dai a kan sarrafa shi a ci shi haka nan. Bayan haka, akan sa shi cikin miya. Kabewa kuwa yadda kabushi ya ke haka kabewa take ita ma a kan dafa ta a ci ta zalla kuma akan sanya ta cikin miya. Nau’in kabushi kuwa akwai babban akwai }arami, ita kabewa haka take ita ma akwai babba akwai }aramar kabewa. Hausawa mazauna Sifawa duk suna amfani da wa]annan kabewa wajen shirya cimaka daban-daban.

## 3.3 KAYAN MARMARI

Kayan Marmari wannan yana nufin irin nau’in kayan marmari da ake samu musamman a ‘yarkasuwa ta garin sifawa. Idan aka ce kayan marmari a nan ko da su ko ba bu su ana iya rayuwa, kaya ne wa]anda sai an koshi ake bi]ar su, a gaskiya a garin Sifawa babu su da yawa domin kowa su ake yi daga wasu wurare domin bu}atar Hausawan garin Sifawa.

### 3.3.1 AYABA

Ayaba tana ]aya daga cikin kayan marmari da rayuwa take bu}ata, kuma zaka same ta a cikin garin na Sifawa a ‘yarkasuwa, sai dai akan kawo ta ne daga wasu birane daban-daban kamar Ibadan da Legos duk suna kawota a garin na sifawa. Harwa yau, akwai ayaba daban-daban kamar haka akwai ayaba wadda ake soyawa da wadda ake ci ba tare da an soya ba, akwai wanda aka busar da ita duk a kan kawo su garin Sifawa a cikin ‘yarkasuwa.

### 3.3.2 LEMUN YAMI

Yana ]aya daga cikin kayan marmari sai dai shi wannan lemun ya sha banban da lemun zaki domin shi yami yake da shi kuma a kan sa shi cikin abinci domin ya bada wani sanadari daban. Bayan haka, lemun yami ana magani da shi, ana kuma amfani da shi wajen wanke duk wani abu wanda ya yi tsatsa ko ya tsufa. A kan yi amfani da shi wajen wannan aikin.

### 3.3.5 LEMUN ZAKI

Lemun zaki shi ma yana cikin kayan marmari musamman ga Hausawa mazauna garin Sifawa da kauyuka suna amfani da shi. Shi wannan lemun zaki da jin sunansa yana da za}i sa~anin lemun yami. Ana amfani da shi wajan sarrafa kayan marmari domin cimaka. Bayan haka akan sha shi hakanan ba tare da an sarrafa shi ba. A gaskiya al'ummar garin Sifawa ba su da ita cen lemun za}i amma a kan kawo shi daga kudancin Najeriya.

### 3.3.6 KARAS

Karas shi ma yana ]aya daga cikin kayan marmari da al'uammar garin Sifawa suke amfani da shi. Shi karas ana amfani da shi wajen sarrafa abinci daban-daban kamar haka akan sa shi cikin shinkafa akan yi miya da shi da sauransu. Bayan haka, akan ci shi ba tare da an ha]a shi da komai ba.

## 3.4 DABBOBI

Babbobi wasu halittu ne da Allah ya bamu domin mu biya wasu bu}atu na rayuwa daban-daban. Allah ya halitta mana su don mu yanka mu ci namansu. Allah ya albarkaci garin Sifawa da kauyukkanta da dabbobi daban-daban. A cikin garin na sifawa, in da ake kawosu a babbar kasuwar garin wato kasuwa wadda tana gaba

da ‘yarkasuwa duk ranar Talata da jumu’ah idan ka zo to zaka sami duk nau’in kalar dabbobin da ka ke so a ranka, sai dai ita ‘yarkasuwa ta garin Sifawa a kan kawo raguna da akuyoyi da kaji amma ba da yawa ba.

### 3.4.1 SHANU

Shanu akwai kalolin shanu da dama da ake samu a cikin garin sifawa, akwai gudale da Bakkwalo da Rahazawa, da Buzuyen shanu duk a kwai su a ‘yar kasuwa garin Sifawa, bayan haka, akan yanke shanu domin a ci namansu ga kuma nono da ake samu ga jikin shanun ga man shanu da ake sanyawa a cikin abinci domin ya }ara masa da]i.

### 3.4.2 RAGUNA

Ana samun raguna daban-daban a cikin ‘yarkasuwa na sayarwa. Ana samun ire-iren raguna a cikin ‘yan kasuwa kamar haka: akwai Balami, da ba’u dan rago duk zaka samu a ‘yarkasuwa ta garin Sifawa.

### 3.4.3 AKUYOYI

Suma akuyoyi suna da tasiri a ‘yarkasuwa ta garin Sifawa, suma Allah ya albarka ce mu da akuyoyi shi ya sa ake kawosu a ko da yaushe a cikin ‘yarkasuwa domin a sayar. Muna da akuya wadda ake cewa yarkasa da ‘yar gida, wato idan aka ce ‘yarkasa da ‘yar gida, wato idan aka ce yar }asa akuyoyi ne wa]anda zaka gan su ba su da girma sosai sai dai suna da }iba kuma basuda tsawo gajeru ne, har wa yau ita akuyar ‘yargida ba ta da }iba kuma tana da tsawo sosai.

### 3.5.4 KAJI

Kaji suma ba’abarsu a baya ba domin annan ake haifuwarsu, harma su yi yawa, saboda yawansu shi zai sa a kawosu ‘yarkasuwa ta garin Sifawa a sayar da su, domin bu}atun yau da kullum.

## 3.6 SUTURA

Sutura tana da mutukar muhaimmanci ga ]an Adam mace ko namiji, domin tana kariya ga ganin tsaraicin mutum. Wannan da wuya a samu kasuwar da ba a sayar da sutura ko dai ta mace ko ta maza, ko wa]anda aka [unka ko wa]anda ba a dunka ba, haka ita ma ‘yarkasuwa ta garin Sifawa ana sayar da sutura da ta mace har zuwa ta maza nau’i daban daban wa]annan sutura Hausawan garin Sifawa

ke amfani da su wajan suturta jikinsu. Ga ka]an daga cikin nau'o'in suturar da ake iya samu su kamar haka: shaddodi da turame da leshi duk a da sauransu duk ana samunsu a 'yarkasuwa ta garin Sifawa.

### 3.5.1 SHADDODI

Shaddodi wani nau'in sutura ce wadda aka sani maza suka fi yawan amfani da ita, amma, mata suma sukan yi amfani da shadda wajen suturarsu, akwai nau'o'in shaddodi da ake samu a 'yarkasuwa kamar shadda galila, da shadda gizna da kuma shadda les da suaransu.

### 3.5.2 ATAMFA

Ita ma atamfa an fi samunta ga matan Hausawa, ita ma akan sameta a 'yarkasuwa ana sayarwa da arha a sa~anin wa]ansu kasuwanni inda zaka sami farashi mai kyau. Akwai nau'in a tamfa daban-daban a cikin 'yarkasuwa kamar haka, akwai ingilish da sufa da wakas da holad da sauransu.

## 3.6 SANA'O'IN DA SUKA YI FICE A KASUWAR

Idan muka dubi ‘yarkasuwa za mu ga cewa, akwai wasu sana’o’in da suka yi fice a cikin kasuwar. Wa]an]an sana’o’in ana yin su ne ba dare ba rana, a kodayaushe za ka samu ana yin wa]annan sana’o’in a ‘yarkasuwa ta garin Sifawa. Ga sana’o’in kamar haka.

### 3.6.1 SANA’AR SAYARDA NAMA (RUNDAWA)

Wannan sana’ar ta sayar da nama a cikin ‘yarkasuwa tana da matukar tasiri ga al’ummar garin Sifawa domin ta wannan hanyar ce al’ummar ke samun abin da suke yankawa su sarrafa su zuwa nama, wa]annan sun ha]a da shanu da raguna da awaki duk suna yankawa a ‘yarkasuwa a garin Sifawa.

### 3.6.2 KAYAN GWARI (KAYAN MIYA)

Wannan sana’a ta sayar da kaayan miya tana taka rawar gani a cikin ‘yarkasuwa domin tana ]aya daga cikin sana’o’in da suka yi fice a ‘yarkasuwa akan sayar da kayan miya daban-daban tun daga tumatur da tarugu da tattasay da albasa da sure da kabushi da kabewa da latas da alayyahu da sauransu duk ana samunsu a cikin ‘yarkasuwa.

### 3.6.3 SANA’AR SAKAI

Idan aka ce sakai, wato duk wani nau'in abincin da ake dafawa za ka same sa wajen masu sana'ar sakai. Wannan sana'a ta sakai tana tafiya a kodayaushe a cikin 'yarkasuwa domin al'umma ba ta rayuwa sai da abinci. Don haka dole a samu musu sayar da abinci a cikin al'umma, wannan sana'a ta sakai ta ha]a da sayar da gero da dawa da masara da maiwa da shinkafa da gya]a da hatsi/damma da sauransu duk a cikin 'yarkasuwa ta garin Sifawa.

### 3.6.4 SANA'AR SHAYI DA BURODI

Wannan sana'ar ta yi fice a cikin 'yarkasuwa domin kodayaushe za ka sami mutane suna sayar da shayi da burodi ko da safe, da rana kai harma da dare suna yin wannan sana'ar ta burodi da shayi. Wannan sana'ar ta sami kar~uwa ga matasa su suka fi yawan yin ta. Bayan haka, sana'ar koli da bulawus mutum ]aya yake yinta, kuma Allah ya yi masa rasuwa tun wannan lokacin wannan sana'a ta koli da bulawus ta ja baya }warai da gaske sai dai idan mutum na son irin wa]annan kayan to sai ya je babbar kasuwa wadda take cikin Bo]inga zai same su.

## 3.7 NA[EWA

Wannan babi na }arshe mai namba 3.7 mai taken na]ewa, wannan babi ya yi bayani irin kayan da ake saye da sayarwa a ‘yarkasuwa a garin Sifawa. Don haka an kasa wannan babin zuwa }ananan sassa daban-daban kamar yadda za mu gani a }asa.

A sashe mai namba 3.0 mai taken shinfi]a wannnan sashen ya yi bayanin }umshiya babin ne a takaice. A sashe mai namba 3.1 yana da taken abinci sun ha]a da shinkafa da gero da masara da dawa da maiwa da hatsi/damma da wake da gya]a. A sashe mai namba 3.2 wannan sashen ya yi bayani ire-iren kayan miya kamar su tamatur da tattasay da tarugu da albasa da sure da alaiyahu da kabushi da kabewa. A sashe mai namba 3.3 yana da taken kayan marmari. A nan sashen ya yi bayani irin su. Ayaba da lemun yami da lemun zaki da yalo da karas. A sashe mai namba 3.4 yana magana a kan dabbobi wa]anda suka ha]a da shanu da raguna da akuyoyi da kaji. A sashe mai namba 3.5 wannan ya yi bayani irin suturar da ake samu a ‘yarkasuwa wanda suka ha]a da: Shaddodi da Atamfofi. A sashe mai namba 3.6.1 sana’o’in da suka yi fice a cikin ‘yarkasuwa ta garin Sifawa wato sayar da nama (rundawa). A sashe mai namba 3.6.2 sana’ar sakai masu sayar da abinci. A sashe mai namba 3.6.4 sana’ar

sayar da shayi da burodi. Daga karshe akwai sashen mai namba 3.7 wato na]ewa wanda ya kawo kunshiya babin a takaice.

# BABI NA HU[U:

## TASIRIN KASUWAR ‘YAR KASUWA A GARIN SIFAWA

### 4.0 SHIMFI[A

Babu shakka ‘yar kasuwa ta garin Sifawa tana da matukar tasiri ga al’ummar garin na Sifawa musamman Hausawa dama wasu }ananan hukumomi da suke kewaye da ita, kai har ma da }auyuka duk suna more wa albarkacin kasuwar ta garin na Sifawa wato ‘yar kasuwa. Wa]annan }ananan hukumomin sun ha]a da }aramar hukumar Shagari da }aramar hukumar Yabo da }aramar hukumar Sanyinna duk su kan zo su kawo kayansu domin sayarwa kama su saya su koma da su garuruwansu. Idan aka ce }auyuka kuwa sun ha]a da Lawazobe duk sukan zo domin saye da sayarwa a cikin ‘yar kasuwa a garin Sifawa.

Bayan haka wannan sashe na hu]u ya }unshi sassa daban daban a cikinsa kamar yanda za mu gani, sashe mai lamba 4.0, shimfi]a, 4.1 amfanin da ake samu a cikin kasuwar, sai sashe mai lamba 4.1.1 ana shigowa da abubuwan da babu su a cikin kasuwar garin sai sashe mai lamba 4.1.2 matasa suna samun aikin yi a cikin

kasuwar, sai sashe mai lamba 4.1.3 tasirin ‘yar kasuwa da ci gaban garin Sifawa baki ]aya.

## 4.1 AMFANI DA AKE SAMU A CIKIN KASUWAR

A gaskiya akwai amfani da ake samu a ‘yar kasuwa, na farko shi ne a duk lokacin da ka zo za ka samu kasuwar a bu]e ana saye da sayarwa a cikinta ba dare ba rana. Na biyu shi ne matasa suna kasuwanci sosai a cikinta suna dogaro da kansu.

Bayan haka ana samun ku]in shiga ga mutane masu zuwa da wanda suke sana’a a cikin kasuwar ta garin Sifawa wato ‘yar kasuwa. Wannan ko shakka babu ya taimaka wajen kawo ci gaba da bun}asa tattalin arzikin Hausawa mazauna garin Sifawa da }ewaye.

## 4.1.3 ANA SHIGOWA DA ABUBUWAN DA BA BU SU A CIKIN KASUWAR GARIN

Misali kayan masarufi gaskiya ne akwai abubuwa da dama da ake shigowa da su a cikin ‘yar kasuwa wa]anda babu su a garin sai dai a kawo mata, wa]annan abubuwa sun ha]a da kayan marmari kamar ayaba da lemu da gwadda da abarba, wa]annan kayan marmari kawo su ake yi. A hannu ]aya ana sayar da kayan hatsi

kamar gero da masara da dawa da sauransu ga masaya domin kaiwa garuruwansu da basu da noman wa]annan kayan abinci.

### 4.1.4 MATASA SUNA SAMUN AIKIN YI A CIKIN KASUWAR

Matasa sune manyan gobe, a gaskiya matasan garin Sifawa har ma da na makwabta suna samun abin yi a cikin ‘yar kasuwa domin akwai masu saya da sayarwa, wannan ya harfar da samun riba ga matasa tare da hana zaman kashe wando. Wasu suna tsaron shago idan za su wuce a biya su aikin yini wasu ko suna yin dako wato }ofar kaya daga wani wuri zuwa wani wuri, idan suka kai sai a biya su ku]in su. Duk wa]annan hanyoyi ne da matasa ke samun ku]in shiga domin rage ra]a]in talauci. Wa]annan ku]a]e da suke samu suna amfani da su wajen hidimominsu na yau da kullum.

### 4.1.3 CI GABAN GARIN SIFAWA

A gaskiya idan aka ce gari ya bun}asa to sai da kasuwanci, idan muka dubi garuruwan da suka ci gaba kamar Kano da Legas duk sun ci gaba ne ta hanyar kasuwanci da suke yi, saboda haka ‘yar kasuwa ta garin Sifawa ta kawo ci gaba sosai a cikin garin na Sifawa domin ta yi suna sosai ta gefen kasuwanci. Bayan haka idan matasa

suna samun aikin yi, zaman banza zai ragu sosai a cikin al'umma, mutane za su shigo cikin garin na Sifawa domin kasuwanci. Wannan kasuwanci ya kawo ha]aka ta mutane daban-daban a cikin kasuwar. Wannan kuwa yana }ara dankon zumunci a tsakanin mutanen gari da 'yan kasuwa wanda kan haifar da abokantaka  a tsakaninsu.

## 4.2 MATSALOLIN 'YAR KASUWA

A gaskiya akwai matsaloli da yawa wa]anda suke damuwar 'yar kasuwa a garin Sifawa. Misali rashin wutar NEPA da rashin samun tallafi daga gwamnati da rashin ofishin 'yan sanda a cikin kasuwar da rashin ruwan fanfo duk wa]annan matsaloli ne da suke ciwa 'yar kasuwa tuwo a }warya.

### 4.2.1 RASHIN WUTAR NEPA (Lantarki)

A gaskiya babu wutar NEFA a cikin kasuwar tun lokacin da ta fara ci har ila yau, idan dai kaga wutar to ka tabbata injin ne aka tada, amma ba wutar NEPA ba. Wannan matsalar ta kawo cikas ga wasu sana'o'in mazauna Sifawa. Don haka samun wutar zai iya inganta sana'o'insu da }ara yawaitar sana'o'i ta yadda za su }ara bun}asa tattalin arzikinsu.

### 4.2.2 RASHIN TALLAFI DAGA GWAMNATI

Inda gwamnati tana tallafa wa 'yan kasuwar garin Sifawa da gaskiya abin ya }ara ha~aka. Amma abin ba haka ba, gwamnati ba ta damu da komai ba, shi ya sa babu duk wa]annan abubuwa da muka lisafo babu su a 'yan kasuwar ta garin Sifawa. Don haka akwai bu}atar gina shaguna da runfuna na 'yan kasuwa. Domin a yanzu idan ana ruwan sama litas wasu 'yan kasuwan su tashi domin gudun kada kayansu su lalace.

### 4.2.3 RASHIN RUWAN FANFO

Babu ruwan fanfo a cikin kasuwar ta garin Sifawa, wannan matsala tana kawo wa kasuwar ci baya idan kaga ruwa to ka tabbata sayensu aka yi, amma ba ruwan fanfo ba. Wannan yana kawo koma baya a ci gaban kasuwanci, domin ruwa sune rayuwa baki ]aya sai da su a ke rayuwa. Ya kamata gwamnati ta taimaka masu a jawo ruwa a ko'ina a cikin kasuwar idan haka bai samu ba to ta sa a yi rijiyoyin murtsatse za su taimaka wa jama'ar da suke kasuwanci a cikin 'yar kasuwa ta garin Sifawa.

### 4.2.4 RASHIN OFISHIN YAN SANDA A CIKIN KASUWAR

A gaskiya rashin ofishin ‘yan sanda a cikin kasuwa yakan kawo matsaloli masu yawan gaske. Na farko za a sami yawan fa]ace-fa]ace a cikin kasuwar na biyu kuwa yawan sace-sace zai yi yawa ga kuma rigingimu da suke iya tasowa a cikin kasuwar tsakanin masu kasuwanci. A nan inda akwai ofishin ‘yan sanda da abin zai yi dama }warai da gaske, samar da wannan zai taimaka wajen kwantar ma ‘yan kasuwar hankali su yi kasuwancinsu a cikin kwanciyar hankali ba tare da tunanin rashin tsaro ba.

### 4.3 NA[EWA

A }arshe wannan babi ya ta}aita duk abubuwan da aka yi a ta}aice kamar yadda za mu gani a sashen farko mai lamba 4.0 shi ne shimfi]a, sai sashe mai lamba 4.1 amfanin da ake samu a cikin kasuwar, sai sashe mai lamba 4.1.2 matasa suna samun aikin yi a cikin kasuwar, sai sashe mai lamba 4.2 matsalolin ‘yar kasuwa, sai sashe mai lamba 4.2.1 rashin wutar NEFA, sai sashe mai lamba 4.2.2 rashin samun tallafi daga gwamnati, sai sashe mai lamba 4.2.3 rashin ofishin ‘yan sanda a cikin kasuwar, sai sashe lamba 4.2.4 rashin

ruwan fanfo sai sashe na }arshe mai lamba 4.2.5 shi ne na]ewa, inda aka tattaro zantukan da aka tattauna a cikin babin amma a ta}aice.

# BABI NA BIYAR

# TA{AITAWA DA KAMMALAWA

## 5.0 SHIMFI[A

Wannan babi na biyar mai taken ta}aitawa da kammalawa zai yi }o}arin bayanin duk abubuwan da suke cikin babin na biyar, bayan haka wannan babi na biyar shi ne }arshen binciken wannan aikin da aka gabatar game da abin da ya shafi tasirin ‘yar kasuwa ga Hausawa da ke garin Sifawa. Wannan sashe na biyar an kasa shi zuwa sassa daban-daban kamar haka. A sashe mai lamba 5.0 mai suna shimfi]a, wannan sashe zai yi }o}arin kawo }umshiyar babin ne a ta}aice. A sashe mai lamba 5.1 mai taken ta}aitawa, wannan sashe zai yi }o}arin tattaro duk bayanai da suka gabata tun farko har }arshe, amma a ta}aice. A sashe mai lamba 5.2 mai taken kammalawa sashe zai yi }o}arin kawo kammalallen bayanai ne game da binciken baki ]aya.

## 5.1 TA{AITAWA

Kamar yadda aka fa]a a farko cewa zai tsakalo bitar ayukkan da ka gabatar cikin wannan bincike amma a ta}aice. A babi na farko 1.0 mai suna gabatarwa, a }ar}ashin wannan sashe an kasa shi sassa-

sassa har guda biyar. A sashe na farko mai lamba 1.0 yana da suna shimfi]a sai sashe mai lamba 1.1 mai suna Bitar ayukan da suka gabata a nan an yi }o}arin bitar muhimman ayukka masu dangantaka da aikin. Sai sashe mai lamba 1.2 mai suna Hujjar ci gaba da bincike inda aka kawo hujjojin ci gaba da wannan bincike. Sai sashe mai lamba 1.3 mai taken Hanyoyin gudanar da bincike, a nan an yi bayani dabarun da aka yi amfani da su wurin gudanar da wannan bincike.

Bayan haka sai sashe mai lamba 1.4 mai suna muhalin bincike a nan an kawo farfajiyar bincike watau fa]in bincike. A sashe mai lamba 1.5 mai suna manufar bincike a nan an yi bayani dalilan aiwatar da wannan bincike. A sashe mai lamba 1.6 mai taken na]ewa, wanda ya tattauna }umshiyar babin a ta}aice.

A babi na biyu kuwa, wannan babi yana da taken takaittaccen tarihin 'yar kasuwa. Wannan babi yana da sassa daban-daban a cikin sa kamar haka: sashe mai lamba 2.0 mai taken shimfi]a, an kawo }unshiyar babin a ta}aice. A sashe mai lamba 2.1 mai suna tarihin garin Sifawa a ta}aice, an kawo tarihin garin Sifawa a ta}aice. Har wa yau a sashe mai lamba 2.2 mai suna ma'anar 'yar kasuwa sai

sashe mai lamba 2.3 mai suna dalilan zuwan cin kasuwar. A sashe mai lamba 2.4 mai taken garuruwa ko }auyukan da ke cin ‘yar kasuwa. Daga }arshe wannan babi ya karasa da na]ewa mai lamba 2.5 inda aka kawo }umshiyar babin a ta}aice..

A babi na uku kuwa, wannan babi yana da suna: Nau’o’in kayan da ake saya da sayarwa a ‘yar kasuwa. Wannan sashe yana da sassa daban-daban a cikinsa kamar haka. A sashe mai lamba 3.0 mai taken shimfi]a. Sai sashe mai lamba 3.1 mai suna kayan abinci. Sai sashe mai lamba 3.1.1 mai suna shinkafa. A sashe mai lamba 3.1.2 mai suna gero. Sai sashe mai lamba 3.1.3 mai suna Masara. A sashe mai lamba 3.1.4 mai suna Dawa. Sai sashe mai lamba 3.1.5 mai taken Maiwa. Sai kuma sashe mai lamba 3.1.6 mai taken Hatsi/Damma. Sai sashe mai lamba 3.1.7 mai suna Wake. A sashe mai lamba 3.1.8 mai taken Gya]a. A sashe mai lamba 3.2 mai taken kayan miya. Sai sashe mai lamba 3.2.1 mai suna tumatur. A sashe mai lamba 3.2.2 kuwa mai suna tattasai. A sashe mai lamba 3.2.3 mai taken tarugu. Sai sashe mai lamba 3.2.4 wato albasa. A sashe mai lamba 3.2.5 mai taken Alayyahu. Sai sashe mai lamba 3.2.6 mai suna sure. A sashe mai lamba 3.2.7 mai suna kabushi/kabewa. A

sashe mai lamba 3.3 mai taken kayan marmari. A sashe mai lamba 3.3.1 mai suna Ayaba. Sai sashe mai lamba 3.3.2 wadda ake wa take da lemun yami. Sai sashe mai lamba 3.3.3 mai suna lemun zaki. A sashe mai lamba 3.3.4 mai taken karas. Sai a sashe mai lamba 3.4 mai taken dabbobi. A sashe mai lamba 3.4.1 mai taken shanu. Sai sashe mai lamba 3.4.2 mai suna raguna. A sashe mai lamba 3.4.3 mai suna akuyoyi. A sashe mai lamba 3.4.4 mai taken kaji. A sashe mai lamba 3.5 mai suna Sutura. Sai a sashe mai lamba 3.5.1 mai taken shaddodi. A sashe mai lamba 3.5.2 mai suna atanfa. A sashe mai lamba 3.6 mai suna sana'o'in da suka yi fice a kasuwar. A sashe mai lamba 3.6.1 mai taken sana'ar sayarda nama (kundawa). A sashe mai lamba 3.6.2 mai suna sana'a sana'ar sakai. A sashe mai lamba 3.6.3 mai suna kamar haka sana'ar shayi da burodi sai sashe }arshe mai lamba 3.7 mai take na]ewa.

## 5.2 KAMMALAWA

Sanin kowa ne cewa duk abinda aka fara za'a cimma }arshensa, wannan jawabin haka yake domin wannan nazarin mai taken "Tasirin 'Yar kasuwa a garin Sifawa". Ya zo kan iyaka domin

Allah cikin ikonsa ya kawo }arshen binciken wanda za a yi jawabi na kammalawa a kan wannan aikin.

Wannan nazarin ya tattaro abubuwa da dama da suke da ala}a da tarihin garin Sifawa. A cikin ]an }aramin kundin an yi bayani a kan ma'anar 'yar kasuwa haka ma an yi bayani garuruwan da ke zuwa cin kasuwar. Ta ~angaren da aikin ya nazarta don }ara ba da haske a kan binciken aikin ya dubi irin kayan abinci da ake sayarwa a kasuwar 'yar kasuwar Sifawa kamar su shinkafa, gero, dawa, masara, maiwa, hatsi, damma, wake da kuma gya]a.

A ~angaren kayan miya kuma wannan kundin ya yi nazari a kan irinsu; tomaturi, tattasai, tarugu, albasa, alayyahu, sure, da kuma kabushi. Ta ~angaren kayan marmari kuwa kundin ya yi nazari a kan irinsu; ayaba, lemun zaki, da kuma lemun yami, yalo, da karas.

Wannan binciken bai tsaya kawai a kan kayan abinci da kayan miya ko marmari ba kawai binciken ya ha]a har da fannin dabbobi kamar su shanu, raguna, akuyoyi da kuma kaji. Ta ~angaren sutura ma ba a manta da ita ba domin kuwa an kallo wannan sashe inda aka kawo shaddodi da atamfofi da sauran kayan tufafi daban-daban. Wannan bincike ya yi nazari akan ire-iren kayan da suka fi fice daga

cikin kayan a nan an dubi irinsu rundawa masu sai da nama, da kayan gwari haka ma masu sana'ar sakai, sai kuma masu sana'ar sayar da shayi da burodi. {undin ya yi nazarin irin amfanin da ake samu a kasuwar Sifawa kamar samun abubuwan da babu su a garin haka ma matasan garin na samun ayyukan yi domin cigaban garin. Haka ma aikin ya kalli matsalolin kasuwar kamar su rashin wuta da rashin tallafin gwamnati da rashin ofishin 'yan sanda a cikin kasuwa da kuma ruwan fanfo.

A }arshe za a iya fahimtar cewa wannan nazari ya yi }o}arin bayanin irin muhimmancin 'yar kasuwa da ke garin Sifawa wajen bun}asa tattalin arzikin al'ummar Hausawa mazauna garin na Sifawa da kewaye. Ba shakka irin wannan nazari yana da muhimmanci wajen za}ulo dabaru daban-daban na kasuwanci domin samun ci gaban al'umma. A hannu ]aya kuwa irin wannan nazari na iya sanya a fiddo da wasu matsaloli da suke addajar kasuwanci ta yadda al'umma za ta samu ci gaban bun}asar tattalin arzikinta.

# MANAZARTA

Abdullahi, M.S. (2000). Tarihin Garin Sifawa Sakkwato: Sifawa Printing Press.

Abdullahi, A.B. (2008). “Kasuwanci A Ma’aunin Karin Magana”. Kundin Neman Digiri na Farko, Jami’ar Usmanu [anfodiyo, Sakkwato.

Adamu, Z. da wasu (2010). “Hausar Wasu ke Babban Sana’o’in Hausawa Kuli da Awo”. Kundin B.A Hausa, Sashen Nazarin Harsunan Najeriya na Jami’ar Usmanu [anfodiyo Sakkwato.

Aliyu, B. (2011). “Harshen Kasuwanci na Gida da na Ba}i a Kasuwar Albasa ta Aleru”. Kundin B.A Hausa, Kundin B.A Hausa, Sashen Nazarin Harsunan Najeriya Jami’ar Usmanu [anfodiyo Sakkwato.

Anka, A. da Muhammad, A. (2005). Zamani Zo Mu Tafi: Nazarin Sababbin Kalmomin Hausa. Kundin Neman Digiri na Farko a Jami’ar Usmanu [anfodiyo Sakkwato.

Bello, S. (2004). “Nazari a kan Kasuwar Kara ta Sakkwato”. Kundin B.A Hausa, Sashen Nazarin Harsunan Najeriya na Jami’ar Usmanu [anfodiyo Sakkwato.

Gali, A. (1986). “Kasuwanci Da da na Ynzu a Birnin Kano”. Kundin B.A Hausa, Sashen Nazarin Harsunan Najeriya na Jami’ar Usmanu [anfodiyo Sakkwato.

Umar, M.M. (2005). “Kasuwanci Muhimmancinsa ga Al’ummar Hausawa”. Kundin B.A Hausa, Sashen Nazarin Harsunan Najeriya na Jami’ar Usmanu [anfodiyo Sakkwato.

Yakasai, S.A. (2006). Darasin ALH 205 Hausa Morphology Lecture 6 Hanyoyin {ir}irar Kalma a Hausa.

## WADANDA AKA HIRA DA SU

Hira da Baba Ummaru Ramen Shuka, Tsoho wanda ya ga yau ya ga jiya, (ka]an mai albarka) Baba Shaba a kasuwar Minimat. Jami'ar Usmanu [anfodiyo, Sakkwato.

Hira da Alh. Sa'adu Muhammad Sani (Chairman na wannan kauwa ta Minimat. Jami'ar Usmanu [anfodiyo, Sakkwato.

Hira da Alh. Bashiru Mai Kayan Sanyi mai La}abi da Suna "[an Basir". Jami'ar Usmanu [anfodiyo, Sakkwato.